

Can dauri, cikin garin da ake kira Sabuwa, an yi wani mutum da ake kiran shi Mammani, yana tare da matarsa mai sunan Rumanatu. Sun haifi ɗiya mata shida.



Lokacin dɑ Rumanatu take ɗauke da cikinta na bakwai, Mammani ya ce mata. "Idan kika haifi ɗiya mace, to kar ki komo gidan nan amma in kin haifi ɗa namiji to, za na shirya maki babbar walima!"



Lokacin da haifuwar ta zo, Rumanatu ta je wajen Fatuma. Ta tambaye ta ɗa namiji ne ko ɗiya mace ce za ta haifuwa?



18/02/2022 11:48



Ta haifi ɗiya biyu : namiji da mace. Ta raɗa wa namijin sunan Hasan, ita kuma mace Usaina. Idan ta kalli Hasan sai ta ji daɗi. Amma idan ta kalli Usaina, sai ranta ya ɓaci. Sai ta yi tunanin, abu guda ya rage ta yi.



Rumanatu ta bari Usaina ga hannun Fatuma kuma ta kai wa mijinta Hasan.



18/02/2022 11:48



Cikin jin daɗi ta gwada wa mijinta jaririn namiji. Ya ji daɗi kuma ya gayyaci dukan mutanen garinsu su zo wajen walimar bikin ɗansa.



Rumanatu.pdf 8



Hasan ya girma kuma ya zama kyakkyawan saurayi. Ita ma Usaina ta girma kuma ta zama budurwa mai ɗan karen kyau.



18/02/2022 11:48



Wata rana, Hasan yana yin kiyon bisashen babansa, sai ya hango wata budurwa mai kyau. "Wannan budurwa ita nake so in aura," ya faɗi.



Ko da ya tambayi aurenta sai ta fara waƙa kamar haka: "Mukhwana wefwe, Mukhwana. So yakhupa omunwa, Mukhwana. Nebebula omukhana, Mukhwana. Barulaka khulwanda, Mukhwana. Nebebula omusiani, Mukhwana. Barera mungo muno, Mukhwana. Iyeyi yakwa, Mukhwana. Iyindi yakwa, Mukhwana."



18/02/2022 11:48



Kullum ana haka, ana haka. Hasan ba ya sani abin da za ya yi ba. Sai ya je wurin uwarsa, Rumanatu, ya faɗa mata. "Na samu wata budurwa mai kyau, kuma ina son auren ta. Amma kodayaushe na tambaye ta sai ta yi ta mani waƙa."



Cikin mamaki, Rumanatu ta ce masa, "abin da yarinyar ta faɗa cikin waƙarta gaskiya ne, ƙanwarka ce. Ku, tawaye ne. Baabanka yana son in haifi ɗa namiji ba ɗiya mace ba. Sai na bari ƙanwarka wajen Fatuma, kai kuma in kawo ka gida wajen babanka."



18/02/2022 11:48



Lokacin da Hasan ya bayyana wa babansa abin da ya faru, sai ya gane rishin gaskiyarsa. Ya kiranyo Rumanatu kuma suka tafi tare gidan Fatuma neman Mariyama.



Lokacin da Mariyama ta dawo gida, babanta da mutanen garin, sun yanka akuya don yin shagalin bikin haɗa kan Usaina da sauren yan uwanta bakwai maza da mata.



18/02/2022 11:48



Bayan shekara ɗaya, Usaina ta auri ɗan wani mai kuɗin ƙauyen. Ta kawo wa uwayenta arziki dayawa tare da jin daɗi.